# Bayanin YADDA

RESOURCE & SUPPORT HUB

UKaid from the British people

## Yadda za'ayi la'akari da **harshe** a lokacin binciken ci da gumi, cin zarafi da barazana ta hanyar jima'i (SEAH)

Ga CSOs da masu bincike a yanayin taimakon agaji ko na ci-gaba

## Me ya sa harshe yake da mahimmanci?

- Harshe wani bangare ne na kowane bincike ko sa ido da kimantawa, amma ya fi mahimmanci musamman a binciken batutuwa masu sirri da jinsi kamar ci da gumi, cin zarafi da barazana ta hanyar jima'i (SEAH).
- A kowace al'umma, kalmomin da muke amfani da su wajen maganar jima'i da tashin hankali sun bambanta tsakanin jinsi, tsakanin sa'anni da rukunai jama'a masu matsayi daban-daban da kuma dangane da wadanda muke magana da su.
- Idan har masu bincike basu shiryawa da maida hankali ga wadancan bambancin, za su iya rasa bayani mai mahimmanci game da abubuwan da mutane suke fuskanta, bukatu da abubuwan da suke so.

Wannan takaitaccen jagora na ba da matakai masu yiwuwa wanda masu bincike da ma'aikata na shirye-shirye suke iya dauka don shawo kan cikas na harshe a binciken su na Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH da sa ido.



## Menene zai iya faruwa mara kyau kuma yaya za'a tabbatar bai faru ba.

Sadarwa za ta iya yankewa:

- Idan anyi binciken a **harshe ko yare** wanda mahalartan ba sa fahimta sosai ko ba sa jin dadinsa, ko wanda yake wariyar mutane masu kwarewa da ilimi mai amfani.
- Idan mai binciken na amfani da kalmomi wanda mahalartar ba sa jin dadinsu, saboda suna dauke da **kyama ko sun sabawa al'adu.**
- Idan mai binciken na amfani da **kalmomi** wadanda mahalartan ba sa fahimta ko kuma suna fahimtarsa daban.

Mafi karanci, ya kamata masu binciken su:

- ✓ Fahimci harsunan da mutane suke magana da su.
- ✓ Fahimci wadansu kalmomi da asali aka fi so da ma'anoni wadanda mahalarta suke amfani da su wajen tattauna batutuwa.
- ✓ Fahimci wadane kalmomi da ma'anoni ne na sirri kuma ya kamata a kauce musu.
- ✓ Kar a yi tsammanin cewa mutane na da fahimta iri daya ta kalmomin da ake amfani da su.
- ✓ Dauki lokaci da fari don bayani akan kalmomi da ma'anonin da ake amfani da su don tabbatar da duk kuna nufin abu daya.

Akwati. 1 [Bincike tare da 'yan gudun hijira na Rohingya a Bangladesh] sun gano cewa ra'ayoyi masu karfi game da harshe da ya kamata mata da 'yan mata su yi amfani da su ya hana ma'aikatan agaji daga fahimtar rahotannin cin zarafi ta hanyar jima'i. Wasu kalmomi sun sabawa al'adu kawai, saboda haka mata da 'yan mata na iya amfani da wasu kalmomi daban kamar "batawa", "zalunci" da "zubar da mutunci" da nufin nau'i daban-daban na cin zarafi. Ma'aikatan agaji na gida sun fahimci kalmomin amma ba asalin ma'anarsu ba, kuma don haka ba'a bayar da rahotonsu ba kuma matan

## Ka'idodi

**Yi magana da harshen mutanen da kuke so ku ji daga garesu**

- Bincike akan Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH na buƙatar mai da hankali musamman ga masu magana da harsuna marasa rinjaye.
- Za ku buƙaci sanin waɗansu harsuna da suke magana da su, ɗauki masu bincike wadanda suke magana da harsunan, kuma fassara kayan aikin bincike zuwa wadancan harsunan.
- Galibi al'ummomi suna da harsuna daban-daban kuma ba kowa da kowa za su yi magana da ko fahimci harshen na ƙasar ko wanda aka fi magana da shi ba.

**Yi amfani da kalmomin da mahalarta suke jin daɗinsu**

- Kalmomin da muke amfani da su ba haka kawai ba. Dabi'unmu na zamantakewa da al'adu ke jagorantar irin kalmomin da muke amfani da su.
- Saboda waɗannan dabi'u sun bambanta, kalma ɗaya na iya nufin abubuwa daban-daban ga mutane daban-daban.
- Wasu kalmomi na nufin hukuncin da aka yanke game da mutane ko ayyukan da suke bayyanawa.  Ana ganin wasu a matsayin da laifi ko bai kamata wasu rukunan mutane kamar mata ko yara su yi amfani da su ba. Wasu kuma sai wasu rukunan mutane ke iya amfani da su kuma yana nuna kasancewa da wadancan rukunan.

**Yi amfani da kalmomin da suke nufin abu ɗaya ga kowa**

- Saboda Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH na iya zama mai wuyar magana akai, galibi muna nesanta kanmu daga wadannan matsalolin ta amfani da ko kalmomin da ba na kai tsaye ba,ko  kalmomi na fasaha kamar kalmomin likitoci, takaita kalmomi, ko kalmomin da suke a wani harshe daban don nufinsu.
- Yana da hadari a yi tsammanin cewa kowa na amfani ko fahimtar wadancan kalmomin bai ɗaya. Don haka yana da mahimmanci musamman a binciken Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH a tabbatar da ma'anonin kalmomin da aka yi amfani da su.

## Yadda za mu tabbatar muna amfani da harshen da ya dace

### 1. Wane harshe mutane suke magana da shi?

- Nemi waɗansu harsunan da mutane suke magana da su. Mutanen gari (ba shugabannin al'umma kawai ba) sune hanya mafi kyau na samun bayani akan wannan. Tabbatar kun yi tuntuba sosai don gano mafificin waɗanda ba'a jin muryoyinsu suke so. Duba akwati 2 a ƙasa don hanyoyin samun bayanai.
- Hada da mutane masu nakasa a lokacin tattaunawa akan harsunan da mutane suke magana da su, kuma nemi ra'ayoyinsu akan hanyoyin sadarwa da suka fi dacewa da bincikenka. Waɗannan za su iya hadawa da fassarar maganar kurma, fassarar bayanin bidiyo, da amfani da hotuna maimakon kayan aikin bincike na rubutu. Ba tare da la'akari da waɗannan ba, basirarsu da abubuwan da suka fuskanta da suka shafi kiyayewa da Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH ba kasafai ake jin su ba.
- Ku sani cewa yadda muke magana da kalmomin da harshen da muke amfani da su na cikin yadda muke tabbatar da mu su waye. Don haka, suna nuna bambancinmu da sauran mutane kuma yana iya rage aminci da tausayawa. Inda yake akwai tarihin rikici ko tashin hankali tsakanin al'ummomi, harshen da “ba daidai ba" ko yare na iya sa mutumin da ke da niyya mai kyau ya zama kamar barazana, kuma don haka ya toshe hanyar tattaunawa. Wannan wata matsala ce ta musamman idan

batun binciken na da sirri ko yana ɗauke da ƙyama,kamar yadda matsalolin ci da gumi, cin zarafi da barazana ta hanyar jima'i ke yi. Ya kamata a ƙara kula don tabbatar da harshen na da aminci kuma ba zai zama da damuwa ga waɗanda suka tsira ba.

- Ɗauki masu binciken wadanda suke magana da harsunan da mahalarta suka fi so, tare da neman tabbaci daga mutanen garin cewa harshensu da yadda suke magana ana fahimta kuma an amince da shi. Wannan na bawa mahalarta damar magana da kwarin gwiwa kuma su fi jin daɗin magana game da batutuwa na sirri fiye da idan da sai sun dogara akan makwabta ko wasu 'yan'uwan su fadi amsoshinsu[1].
- Yi la'akari ko zai taimaka idan an ɗauki wani daga "waje" tare da tawagar masu bincike don yin tambayoyin da ma'aikatan shirin ba sa iya yi. Wannan zai iya haɗawa da kalubalantar tunanin mahalarta da fari cewa masu aikin agaji ba su da laifin amfani da dama, cin zarafi ko barazana ta hanyar jima'i, ko tambaya game da batutuwa wadanda mahalarta suke shakkar tattaunawa tare da ma'aikatan shirin.
- Horar da tawagarka na bincike su zama a shirye ga matsalolin harshe (duba ƙasa) kuma fassara kayan aiki na binciken zuwa harshen

> **Akwati. 2 Neman waɗansu harsunan da mutane suke magana da su**
>
> Saukar da taswirar harshe kyauta da bayanin harshe na wasu ƙasashe daga [https://translatorswithoutborders.org/language-data/](https://translatorswithoutborders.org/language-data/). Wannan baya ba da bayani na gida, amma zai iya zama hanyar farko ta gano dabarun harshen da ake buƙata don tambayar mutane game da harshen da suka fi so. Idan zai yiwu samu bayani da aka sabunta akan fifikon harshe da sadarwa ga al'ummomi na gida ta hanyar haɗa da [tsayayyun tambayoyi guda huɗu](tsayayyun tambayoyi guda huɗu) a cikin binciken buƙatu da sauran bincike bincike da aka shirya

ko harsunan da suka fi jin daɗin karantawa da amfani wajen yin ganawar.

## 2. Waɗanne kalmomi ya kamata mu yi amfani da su?

A lokacin shirya binciken, ɗauki lokaci tare da tawagar bincike don tunani da tattaunawa game da cikas na sadarwa masu yiwuwa. Yi shirin tattauna batun kalmomi a lokacin horon kafin fara binciken. Kuyi maganar kalmomi da ma'anoni da suke iya zama masu sirri tare da masu taimakawa yin bincike a lokacin horon, don samun ra'ayoyinsu da jawo hankalinsu ga abubuwan da za su iya zama da sirri.

- Shirya jerin kalmomi da ma'anoni da aka yi amfani da su a kayan aiki na binciken, da kalmomi da ma'anoni game da batun na binciken wadanda za su iya tasowa a lokacin tattaunawa tsakanin tawagar bincike da mahalarta.
- Tattauna waɗannan kalmomin da ma'anonin tare da tawagar masu bincike. Fara da jera maganganu daban-daban cewa rukunai jama'a daban-daban za su iya amfani da su a harsunan da suka dace da abin da kowace kalma ta kunsa, dangane da wadanda ake magana da shi. Za ku iya amfani da wani misali kamar jinin al'ada / haila / jinin haila / lokacin wata don ba da misali.
- Yi tunani game da kalmomi da kalmomin izza da mahalarta ke iya amfani da su ko suka fi so. Waɗansu kalmomi ne suke da sosa rai? Waɗanne kalmomi za su iya jawo kunya ko fushi tsakanin mahalartan? Waɗanne kalmomi ya kamata a kauce musu? Waɗanne fassara ga duk wadannan kalmomin za su fi daidai kuma za'a fahimta nan da nan? Waɗanne kalmomi suke samar da muhalli mai aminci? Wannan yana da mahimmanci musamman a lokacin mu'amala da waɗanda suka tsira daga Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH ko duk masu alaƙa.
- Tattauna wadanne kalmomi suke da wuya ga masu taimakawa ga bincike su yi amfani da su

---

[1] Yi hankali a lokacin magana game da batutuwa na sirri kamar ɗaukan masu binciken Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH daga cikin al'ummar zai iya zama da haɗari ga sirri. Za ka iya tunanin ɗaukan masu bincike wadanda ba su fito daga cikin al'ummar ba don kare sirri.

saboda za'ayi tunanin ba su da kunya ko za su iya fuskantar matsaloli a cikin al'umma bayan binciken.

- Shirya jerin kalmomin da kuke iya amfani da su da waɗanda ba kwa iya amfani da su. Koma ga wannan don gyara kayan aikin binciken kafin gwaji.
- Gano kalmomi ko takaitatun kalmomi wanda suke buƙatar a ba da ma'anarsu ga mahalarta. Waɗansu kalmomi za su kasance sabbi ga mahalarta kuma za su buƙaci ba da ma'ana?
- Mai da hankali musamman ga abubuwan sirri game da kalmomi da ma'anonin a lokacin gwada kayan aikinku na bincike. Ba da lokacin gyara kalmomin da aka yi amfani da su a kayan aikin naku bisa ga gwajin kuma don bayyanawa tawagar masu bincike akan

Idan kalmar "fyaɗe" a cikin harshen da ya dacean taba amfani da ita kawai da nufin tursasawa ta hanyar jima'i na namiji akan mace, ba za ta zama kalmar da ta dace a yi amfani da ita ba don tattaunawar tashin hankali akan maza da yara maza ba. Wata kila za ku buƙaci tattaunawa akan wata kalma daban, misali "azabtarwa", wdnda mahalarta za su fi iya alakanta ta da fyaɗe na maza.

kalmomi mafiya kyau da za'a yi amfani da su (duba akwatin a ƙasa).

### 3. Yadda za'a gabatar da waɗannan kalmomin a lokacin tattara bayanai?

- A lokacin ganawa da tattaunawa na gungu, yiwa mahalarta bayani cewa za ku iya amfani da wasu kalmomi a bayyane kuma hakan ba wai da nufin kunyata ko zagin kowa ba. Yi bayani cewa za ku yi amfani da waɗannan kalmomin don ƙara fahimta kuma cewa a tare za ku iya amincewa akan kalmomin da za'a yi amfani da su a lokacin ganawar ko tattaunawar yadda kowa da kowa za su sake da shi.
- Gabatar da kalmomin da kanka maimakon tambayar mahalartan su faɗe su. Tambayi mahalartar idan suna jin daidai idan mai binciken yayi amfani da wannan kalmar a lokacin aikin bincike. Tambaye su idan su kansu za su ji daidai wajen amfani da kalmar a lokacin aikin binciken. Idan sun amsa "a'a" ga kowace ɗaya daga cikin waɗannan tambayoyin, tambaye su ko akwai wata kalma daban wadda za su fi so a yi amfani da ita ga wannan. Zama a shirye don ba da shawarar

Wata kila mahalarta ba za su yi la'akari da shi "ci da gumi ta hanyar jima'i" ba idan wani ma'aikacin agaji yayi jima'i da wata daga cikin al'ummar da abin ya shafa don samun kyaututtuka ko fifikon samun damar taimakon agaji. A irin wancan yanayin za ku iya tambayarsu yaya mutane suke kiran wancan yanayin, kuma ku amince da amfani da waccan

wasu kalmomi daban idan mahalartan suna jin kunya ko ba su da wata shawara.

- Za ku iya farawa da kalmar "rashin da'a" kuma kuyi bayani cewa wannan na iya kasancewa da ma'anoni daban-daban. Akwai nau'in rashin ɗa'a da dama, har da ci da gumi, cin zarafi da barazana ta hanyar jima'i, wanda shine bincikenku ke ƙoƙarin fahimta. A yanayi inda kalmomi kamar "jima'i" suka sabawa al'adu, za ku iya amincewa tare da masu taimakawa da binciken cewa za ku yi amfani da kalmar "rashin ɗa'a" da nufin ci da gumi, cin zarafi da barazana ta hanyar jima'i.
- Guji rubuta kowanne daga cikin waɗannan kalmomin akan fallen takarda ko allo, saboda zai iya jawo a cigaba da jin kunya. Kuma zai iya jawo sabanin fahimta ko fushi idan waɗanda ba sa cikin aikin binciken sun ga waɗannan kalmomin; za su iya ma jawo illa ga masu halartar bincikenku.

### 4. Tabbatar fahimtar kowa iri ɗaya ce.

- Ɗauki lokaci wajen yin bayanin bambanci tsakanin Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH da Cin zarafi don banbancin jinsi (GBV) ga mahalarta, da kuma tawagar masu bincike. Galibi Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH wata sabuwar kalma ce ga al'ummomi, kuma mutane za su yi tunani kuna nufin Cin zarafi don banbancin

jinsi wato GBV. Ba'a ma cika sanin takaitacciyar kalmar Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH ba. Bayyana cewa kuna tattauna Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH kuma ba wai illoli da cin zarafi da wata kila suke faruwa a cikin al'ummar gaba-daya ba. Don ƙarin bayani da fatan za'a duba wannan Mujallar RSH wanda ke bayyana bambanci tsakanin Cin zarafi don banbancin jinsi wato GBV da Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH.

- Kada ku yi tsammani cewa mutane na da fahimta ɗaya na kalmomin da ake amfani da su. Masu bincike da mahalartar bincike wata kila za su san takaitacciyar kalma kamar Kariya daga ci da gumi da Cin Zarafi ta hanyar Jima'i wato PSEA ko Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH a manyan harsuna kamar Turanci ko Faransanci, ko da ba asalin harshen da suke magana da shi ba ne. Koda mutane sun ce sun taɓa jin wannan kalmar dama kuma sun san ta, ka da ku yi tsammani cewa kuna da fahimta ɗaya na ma'anarta. Tambaye su su yi bayanin fahimtarsu ta kalmar don tabbatar da kuna magana game da abu ɗaya.
- A yanayi inda mutane suka fi sakewa wajen magana game da ci da gumi, cin zarafi da barazana ta hanyar jima'i a bayyane, zai fi kyau a yi amfani da asalin kalmomin don gudun sabanin fahimta. Wannan zai iya ƙunsar tattaunawa da fari me mutane suka fahimta da “ci da gumi ta hanyar jima'i”, “cin zarafi ta hanyar jima'i” da “tursasawa ta hanyar jima'i”, da kuma amincewa akan takaitaccen bayanin ma'anarsu wanda kowa na iya komawa kansu.
- Haka kuma, wasu kalmomin da ƙungiyarku suke amfani da su don nuna girma, kamar “mai aikin jima'i”, na iya zama abun mamaki ga mahalarta, wanda maimakon shi za su ce “karuwa”. A irin wadancan yanayin za ku buƙaci yin bayanin me ku ke nufi kuma ku amince akan kalmar da kowa zai fahimta don dalilin ganawar.

**Akwati. 3 Yadda za'a gwada fassara kayayyakin aiki na bincike.**

Gwada harshe na gida, fassarar kayayyakin aiki na bincike tare da masu taimakawa da bincike da masu duba ayyukansu don gano wuraren da za su iya jawo rikici ko bambancin fassara kuma tabbatar kowa ya fahimta daidai.

Tambayoyin da za'a yi sun hada da:

- ✓ Me wannan tambayar take nufi?
- ✓ Waɗanne bangarorin tambayar ne ba'a fahimta ba?
- ✓ Waɗanne tambayoyi masu taimakawa da bincike suke iya kasa fahimta?
- ✓ Shin akwai kowacce daga cikin tambayoyin wadda take sa ku jin wani iri?
- ✓ Idan za ku yiwa abokanku ko wani dan'uwanku wannan tambayar, ta yaya za ku yi ta?
- ✓ Shin akwai kalmomi na gida waɗanda za su fi bayyana ma'ánar da kyau?

Tambayi abokan aiki waɗanda ba sa cikin masu tsara ko fassara kayayyakin aiki su maimaita ma'anar rubutun da aka fassara zuwa asalin harshen, kuma duba ko yayi daidai. Yi gyaran da ya dace ba tare da canza asalin ma'anar tambayoyin binciken ba.

A matsayin mataki na karshe, gwada kayayyakin aiki na binciken a cikin jama'ar da ake nufa kuma yi kowane gyara kafin a fara tattara bayanai.

## Karin jagorar RSH akan sa lura, Kimantawa da bincike cikin aminci.

- Shawarwari masu mahimmanci na RSH don gudanar da ziyarar lura cikin aminci
- Rubutun yadda za'a yi: Yadda za'a tsara da aiwatar da ayyukan sa lura, kimantawa da binciken cikin aminci da ɗa'a
- Rubutun yadda za'a gudanar da binciken Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH cikin aminci.

- Bincike: mu sa ya zama da aminci